# DEUTSCHE WELLE
# JI KA KARU

## Aljannar Kare – Haɗarin afkawa cikin bashi
## Kashi na farko: Sabon keke

Wanda ya rubuta: James Muhando
Wanda ya fassara: Ɗanlami Bala Gwammaja
Wadda ta tace: Halima C. Schmaling

**’Yan Wasa:**

| | |
|---|---|
| Mai ba da labari: | ɗan shekara 30 |
| Bash: | ɗan shekara 15 |
| Jamila: | ’yar shekara 15 |
| Ali: | ɗan shekara 15 |
| Wata ɗaliba: | ’yar shekara 14-17 |
| Ligidi: | ɗan shekara 17 |
| Binta: | ’yar shekara 13 |
| Zaliha: | ’yar shekara 35 |
| Direban babbar mota: | ɗan shekara 40 |

**Mai ba da labari:**

Jama'a, muna yi muku marhabin a cikin wani sabon shirin na "Ji Ka Karu" mai suna "Aljannar Kare – Haɗarin afkawa cikin bashi". Ko kuma na ce ina yi muku maraba da zuwa cikin ofishina. Ni dai sunana Aliyu Bello kuma ina aiki ne a wannan ƙayataccen ƙaramin banki a matsayin jami'i mai kula da harkokin ba da bashi. Ni ne kuma zan kasance tare da ku a cikin wannan shiri, amma don Allah ku yi jimurin sauraronmu don kuwa ba zan ɓata muku lokaci wajen cika ku da surutu a kan aikina ba. Kada ku yi mamaki idan na ce da ku ni ma kwanan nan nake kamar ku, surutu kamar saurayin da ya ga budurwa.

An haife ni a wani ƙauye wanda bai fi kilomita 30 daga nan ba mai suna Kwazaye. Lokacin da nake makaranta burina dai shi ne, idan na girma na zama lauya. Ban taɓa tunanin zan zama wani jami'i mai kula da harkar bayar da bashi ba! To, amma kada na yi azarɓaɓi. Bari na yi waiwaye adon tafiya, wato na faro muku labarin tun daga tushe, lokacin da ba a san ni da sunan Aliyu Bello mai kula da harkar bashi ba. A wancan lokacin dai kawai Ali sunana. Yau shekara 15 cif-cif yayin da hutu ya ƙare aka kuma koma makaranta. Lokacin ne na haɗu da 'yan ajinmu Jamila da Bash, suna kuwa cike da labarai da wasu abubuwan mamaki da suka yi min guzurinsu!

**Fitowa ta 1: A makaranta**

| | |
|---|---|
| **Jamila:** | Kai Ali! Ga ni nan! |
| **Ali:** | Jamila! Ga ni nan zuwa! |
| **Jamila:** | Kai! Amma Ali, ka zama wani tumuli. Kalle ka yadda ka zama! |
| **Ali:** | To ke kuma a ce da ke me! Saboda ƙiba ma ga shi awarwaronki har shati ya yi miki. |

**Jamila:** E to, kana da gaskiya!

**Ali:** To, yaya hutun?

**Jamila:** Lafiya. Kai ma dai da ganinka ka ji daɗin hutun nan. Kai! Ali ka ga yadda ka zama wani rusheshe a cikin wata biyu kacal. Me ka dinga ci ne?

**Ali:** Kai! Na ma manta, ai na daina miki magana.

**Jamila:** To! Saboda me kuma?

**Ali:** Wannan ai wulaƙanci ne! Sai ki sulale kawai ki bar gari duk tsawon hutun nan ba ki faɗa mana ba, sannan kuma ki ce muna tare?

**Jamila:** Haba nawan, na san ba za ka riƙe ni da wannan a zuci ba. Yaya labarin Bash kuwa?

**Ali:** Ai sai ki tambaye shi, ga shi can ma ya taho a kan keke. … A'a! Me ya sa kowa yake share ni a 'yan kwanakin nan?

**Jamila:** Wataƙila surutunka ne ya yi yawa! Kai yaron nan! Ga mu nan!

**Bash:** Bash za ki ce! Sunana Bash. Sau nawa zan faɗa miki ki daina kirana Yaro?

**Jamila:** Wannan kai ta shafa!

**Ali:** Iye! Su Bash, an yi sabon keke!

**Jamila:** Keken ma irin na 'sports'!

**Bash:** Ku duba da mai gani mana! Na 'sports' ɗin ma sabon yayin nan, BMX, mai giya goma sha shida!

**Ɗalibi:** Don Allah kalli keken can! Kai!

**Ligidi:** Kai mutumina! Amma keken nan ya yi! Zo nan, ka ba ni in ɗana.

**Mai ba da labari:**
To, a wannan ranar dai abokina Bash ya yi sababbin abokai da yawa, waɗanda suke so su ɗana kekensa. Gaba ɗaya ma sai ya share mu ni da Jamila saboda yana so ya ƙulla abota da irin manyan yaran nan na makaranta. To, ko ina irin wannan abotar za ta? Ma ji wannan daga baya. A kuma can gidanmu da yamma:

**Fitowa ta 2: A gidan su Ali**

**Zaliha:** Kai?! Mts! Wannan yaro! Na sha faɗa masa idan ya taso daga makaranta ya dinga kai jakarsa ɗaki! … Ali! Kai Ali! … Ali! Na san kana jina. Za ka zo, ko sai na zo na janye kunnenka na kawo ka?

**Ali:** Ga ni, Mama!

**Zaliha:** Ga ni, Mama! Mene wannan?

**Ali:** Jakar makaranta ce.

**Zaliha:** Ta waye?

**Ali:** Tawa ce!

**Zaliha:** Me ya kawo ta falo? Me aka ce da ku a kan barin jaka a ko'ina idan kuka taso daga makaranta?

**Ali:** Cewa aka yi kada mu bar su haka ko'ina …

**Zaliha:** Sai a ...

**Ali:** Sai dai mu ajiye su a ɗakinmu a waje guda.

**Zaliha:** To me ya kawo ta nan?

**Ali:** Ni wallahi Mama, na gaji! Kullum fa a ƙasa nake dawowa daga makaranta nan. Duk 'yan makarantarmu kowa yana da keke!

**Binta:** Ni keken ne da ni? Ko ka taɓa ji ina wata magana?!

**Ali:** Ke Binta don Allah, ki rufe mana baki!

**Zaliha:** Ai gaskiyarta. Sai kana da keke za ka dinga kula da kayanka? Ka ga, ɗauke jakar nan daga nan!

**Binta:** Na san abin da ya sa yake wannan fushin, Mama. An saya wa abokin nan nasa Bash sabon keke ne.

**Ali:** To, ke ina ruwanki ne ma ke, daƙiƙiya kawai! 'Yar sa ido.

**Zaliha:** Tooo! Da ma haka abin yake? To wallahi ku saurare ni da kyau! Daga yau, kada ku kuskura ku dinga gasa da waɗansu, kun ji ko? Ko kun san daga gidan da Bash ya fito shi?

**Ali:** Mama, su ma talakawa ne kamar mu fa!

**Zaliha:** Ko ma talakawa ne. Kun kuwa san yawancin matsalolin da muke fama da su sun samo asali ne saboda gasa da muke yi da waɗansu?

**Mai ba da labari:**
Amma ina! Duk ƙoƙarin da babata ta yi don ta fahimtar da ni bai yi wani amfani ba ko kaɗan. Ni dai buƙatata a ce na samu keke ko ta halin ƙaƙa! Haka na kwanta ina fushi. Can da na farka sai na ji kamar muryar babata da kuma sautin ƙararrawar keke:

**Zaliha:** Kai Ali, tashi! Tashi mana, sarkin barci! Ka san fa za ka makara! Ko ka manta ne?

**Ali:** Don Allah, ku ƙyale ni, barci nake ji.

**Zaliha:** Tashi, na sayo maka sabon keke.

**Ali:** Keke! Na gode miki, Mama! Wallahi kuwa, keken ne!

**Mai ba da labari:**
Sai dai kash, wannan fa a mafarki ne. Babban abin takaicin kuma shi ne, ganin da na yi wa ƙanwata yayin da na tashi tana ta sheƙa dariya.

**Ali:** Keke! Ni ina sabon kekena yake?

**Binta:** Za ka makara fa. Wane keke? Mafarki kake yi kasa! … Mama! Mama! Ali yana mafarkin keke!

**Ali:** Don Allah, fice min daga ɗaki! Fita mana! Ba kya ganin abin da aka rubuta? Ga shi nan a bakin ƙofa an rubuta “Ba a shiga”! Ba za ki fita ba?

**Binta:** Ali yana mafarki! Ali yana mafarki!

**Ali:** Mts! Da ma mafarki nake yi ne? Kai!

**Fitowa ta 3: A makaranta**

**Jamila:** Kai Ali tundurki!

**Ali:** Haba Jamila! Me kike so na yi ne don ki daina kirana da wannan sunan?

**Jamila:** Ba komai, sai dai ka dinga yin gudu kullum in za ka taho makaranta.

**Ali:** Har kin tuna min. Mu yi sauri mu nemi Bash. Ya yi alƙawarin zai rage mana hanya a sabon keken nan nashi!

**Jamila:** Ɗan halak, ga shi can …

**Ali:** Wa nake gani suna tare kamar Ligidi?

**Jamila:** Kai, amma da mamaki! Ligidin da kullum sai ya ci zalinmu, ya ce mana tumakai!

**Ali:** Rabu da shi. Kauce mana ma kawai yake yi. Ko kallonmu ma ya ƙi yi.

**Jamila:** Ah! Bash! Bash!

**Ali:** Kauce mana, Jamila! Ba kya gani ma gudunmu yake yi?

**Mai ba da labari:**
Da haka da haka Bash ya share manyan abokansa saboda ya samu Ligidi mai ji da kansa a makaranta. Shi dai Ligidi azzalumi ne, kuma kimanin shekaru uku ke nan babu karkataciyar kukarsa sai waɗannan abokan juna su uku. Ban da cin zalinsu da cutarsu ba abin da yake yi. Sai dai abin da Bash bai sani ba shi ne, Ligidi azzalumi bai iya keke ba.

**Fitowa ta 4: A hanya**

**Ligidi:** Kai, riƙe min keken na hau.

**Bash:** Kamar yaya? Na ɗauka ka iya keke!

**Ligidi:** Na iya mana. So dai kawai nake ka riƙe min na hau.

**Bash:** Ai in da ka iya, da ba za ka ce na riƙe maka ba!

**Ligidi:** Kai! Za ka riƙe min na hau ko ba za ka riƙe min ba?

**Bash:** To, amma don Allah ka yi a hankali!

**Ligidi:** Ban faɗa maka na iya ba! … Kai, yaya ake tsayawa?

**Bash:** Ligidi, ga gingimari nan! Diro Ligidi, diro!

**Direban babbar mota:** Ku daina wasa a kan hanya, shegun yara kawai! Ba wanda ya ji ciwo ko?

**Bash:** Ba mu ji ciwo ba, amma an markaɗe mini kekena.

**Direban babbar mota:** Maganinku ke nan! Yaran banza! Ba kuma zan biya ba!

**Ligidi:** Wai! Saura ƙiris…! Amma na tsorata fa!

**Bash:** Wayyo kekena! Ka ga abin da ka jawo min ko!

**Ligidi:** Sai dai ka yi haƙuri.

**Bash:** Na yi haƙuri? Abin da ma za ka ce mini ke nan? Bashi fa na karɓi keken nan, ban ma gama biyan kuɗin ba tukuna!

**Ligidi:** Na ce maka ka yi haƙuri. Ko ba za ka yi ba?

**Bash:** Duba fa ka gani! Ya ratattake gaba ɗaya! Wayyo kekena!

**Mai ba da labari:**

An markaɗe sabon keken Bash yadda ba zai gyaru ba. Shi kuma ummul haba'isin wannan al'amari ba abin da ya dame shi. Da mu da iyaye da kuma sauran abokan Bash duk mun ɗauka kuɗi ya sa ya sayo keken nan. To, sai daga baya muka gano ashe bashi ya karɓa. Kuma bai ma gama biya ba, ga shi har an markaɗe shi. Daga baya kuma muka ƙara gano cewa ashe abin ma ba a nan ya tsaya ba. Ko me zai biyo baya?

To, bari na dakata haka. Zan kai wa shugabata waɗannan takardun domin ta sa hannu. Amma kuna iya biyo mu don ku ji yadda abin yake a sauran kashe-kashen wannan wasa namu mai suna "Aljannar kare – Haɗarin afkawa cikin

bashi".

Idan kuma kuna son ku sake sauraron wannan shiri, sai ku ziyarci adireshinmu na yanar gizo, wato dw.de/lbe. Kuna iya kuma shiga shafinmu na 'Facebook'. Ku huta lafiya, mun gode.